**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.47 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Alhaji Kassu Zurmi A Matsayin Makaɗin Maza

**Shu'aibu Abdullahi Jangebe**
Sashen Hausa Kwalejin Kimiya Da Fasaha Gusau, Jihar Zamfara

**Corresponding Author: Shu'aibu Abdullahi Jangebe**
Email:
LambarWaya:

**Tsakure**

Kiɗa da waƙa a ƙasar Hausa wani ginshiƙin abu ne da ake aiwatarwa don ilmantarwa ko sadarwa ko nishaɗantarwa ko bayar da wata gudummawa ta musamman. Kusan kiɗa ya yi ruwa, ya yi tsaki sosai a cikin rayuwar Bahaushe, musamman rayuwar da ta dangane da zamantakewa da sana'o'i da bukukuwa da lokutan shaƙatawa. Akwai waƙoƙin baka da yawa waɗanda suka danganci fuskoki daban- daban tun daga na farauta da yaƙe- yaƙe da na sarakuna da na masu sana'o'in gargajiya da na 'yan kasuwa wato attajirai da na masu jaruntaka da na sojoji da na ma'aikatan gwamnati ko wata Hukuma da na Malamai bisa fannoninsu mabambanta da na dabbobi da tsuntsaye da ƙwari da gulabe da garuruwa har zuwa ga waƙoƙin yunwa da fari da na ɓarayi da na 'yan caca da na soyayya da sauransu. Ashe ke nan waƙoƙin baka na Hausa sun yi ruwa da tsaki a ko'ina cikin ɓangarorin rayuwar Hausawa.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Kiɗa da waƙa a ƙasar Hausa wani ginshiƙin abu ne da ake aiwatarwa don ilmantarwa ko sadarwa ko nishaɗantarwa ko bayar da wata gudummawa ta musamman. Kusan kiɗa ya yi ruwa, ya yi tsaki sosai a cikin rayuwar Bahaushe, musamman rayuwar da ta dangane da zamantakewa da sana'o'i da bukukuwa da lokutan shaƙatawa.

Akwai waƙoƙin baka da yawa waɗanda suka danganci fuskoki daban- daban tun daga na farauta da yaƙe- yaƙe da na sarakuna da na masu sana'o'in gargajiya da na 'yan

kasuwa wato attajirai da na masu jaruntaka da na sojoji da na ma'aikatan gwamnati ko wata Hukuma da na Malamai bisa fannoninsu mabambanta da na dabbobi da tsuntsaye da ƙwari da gulabe da garuruwa har zuwa ga waƙoƙin yunwa da fari da na ɓarayi da na 'yan caca da na soyayya da sauransu. Ashe ke nan waƙoƙin baka na Hausa sun yi ruwa da tsaki a ko'ina cikin ɓangarorin rayuwar Hausawa.

Wannan muƙala za ta dubi Alhaji Kassu Zurmi a matsayin makaɗin Maza. Makaɗan maza su ne, masu yi wa jarumai da mayaƙa masu neman suna waƙoƙi. Kassu Zurmi na ɗaya daga cikin irin waɗannan mawaƙan, don haka muƙalar za ta yi nazari a kansa domin zaƙulo bayanai da za su nuna cewa, lalle shi Kassu Zurmi makaɗin maza ne.

## 2.0 Tarihin Kassu Zurmi

An haifi Kassu a wani gari da ake kira Magarya kamin daga bisani ya dawo a ƙauyen Kadawa ta ƙaramar Hukumar Zurmi da ke cikin Jihar Zamfara, a daidai shekara ta 1910. Sunan mahaifinsa Amadu, sunan kakansa kuma Malam Gandau Dumfawa. An yi masa laƙabi da suna Sarkin Fawa Gandau, sunan mahaifiyarsa "Maimuna" wadda ake yima laƙabi da suna Kande 'Yar Gidan Goga.

Sunan Kassu na yanka shi ne Abubakar. Dalilin yi masa wannan laƙabi na Kassu shi ne saboda an haife shi ne a ranar Lahadi kasuwar Dauran, shi ya sa aka yi masa wannan laƙabi watau Kassu kalma ce ma'anar wai mai kasuwa. Asalin Kassu an ce Bagobiri ne, saboda kakanninsa ne Gobirawa. Sun taso daga ƙasar Gobir a wani gari da ake kira Kurawa suka yaɗa zango a wani gari da ake kira "Dumfawa" ta ƙaramar Hukumar Zurmi. Daga nan sai kuma suka tashi daga garin "Dumfawa" suka koma garin "Magarya". Daga garin na "Magarya" kuma suka matsa zuwa wani ƙauye da ake kira "Kadawa" watau "Kwata" duk a cikin ƙaramar hukumar mulki ta Zurmi. Kassu ya nuna haka a cikin waƙar Nomau inda yake cewa:

> "Uban balinɗo, shi ya isheni har Kadawa".

Wannan ya nuna mana cewa shi mutumin Kadawa ne. Kassu Zurmi bai sami damar yin karatun boko na zamani ba, amma ya taɓa karatun Alƙur'ani da sauran littattafai na fiƙihu. (Gusau, 2005) a maƙera ta malan Ladan na garinsu.

Gado, Kassu Zurmi ya gadi kiɗa ne a wajen mahaifinsa. Kassu ya fara bin mahaifinsa wajen kiɗan tun yana yaro ƙarami. Bayan koyon kiɗan da yake yi daga wajen mahaifinsa ya taɓa kiɗan Duma zaune. kiɗan noma, kiɗin bori, fawa, farauta, da ɓarayi, amma bai mayar da hankalinsa sosai a kansa ba kamar na tauri, shi dai kiɗan ya gada, ya taras ubansa yana yi don haka ya himmatu a kansa, har Allah ya bashi rabo mai yawa a ciki.

A matsayinsa na makaɗin farauta da 'yan tauri ba wai gidajensu kawai yake bi idan suna ko biki ya kama ba, a'a tare dashi ake zuwa dajin farauta, duk abin da aka yi na farauta a gaban sa, ba wani mai bashi labari ra'ayul ainu ne shi. Shi kansa a wasu ɗiyan waƙoƙinsa ya nuna cewa da shi ake zuwa farauta dubi abun da yake cewa: (Gusau, 2005)

> "Tahiya makoɗa ko dajin kuna,
> Sa'annan kowaj ji 'yan kalanguna na Jaji na'amadu,
> Sai ɗa da ɗa ka kai nama daji.
> (Waƙar Katakore Jabanda). (Gusau, 2005:225- 226)

Kassu Zurmi yana amfani da kalangu a matsayin abin kiɗansa. Kassu ya yi nau'o'in kaɗe- kaɗe a matsayinsa na makaɗin kalangu. Daga cikinsu akwai kiɗan noma, kiɗan farauta da 'yan tauri, sai kiɗan ɓarayi da 'yan caca.

Kassu Zurmi ya yi aure cike da zuriya mai yawa, ya bar matan aure huɗu waɗanda suka haɗa da: Sa'adiya (Yaya), Jawairiyya (Auta), Aishatau (Karɓa), da Zainab (Abu). Haka kuma, Allah ya azurta shi da 'ya'ya da yawa. Ya bar kimanin ɗiya goma sha biyu shidda maza, shidda mata. Maza sun haɗa da: Umaru ƙaho da Usman da Sani ɗan Gabci da Muhammadu Namakka da Malam Aliyu da Rabi'u. A halin yanzu uku na raye, uku sun rasu. Waɗanda suka rasu su ne: Umaru ƙaho da Usman da Sani ɗan Gabci. Waɗanda ke raye su ne: Muhammadu Namakka da Malam Aliyu da Rabi'u. 'Ya'yansa mata akwai Manga, Salamatu, Raula, Balaraba, Mardiyya da kuma Nana Asma'u, wadda ita ce Auta. Cikin 'ya'ya mata biyu sun rasu, huɗu ne na nan raye, suna aure a gidajen mazansu. Su ne: Raula, da Balaraba, da Mardiyya da Nana Asma'u. (Hira da jikansa, Murtala Usman, 18-12-2024).

Daga cikin manyan 'ya'yansa ne Umaru ya zama makaɗin Tauri. Kusan shi ne mai gadonsu. Amma shi ɗaya ɗan nasa Usman sai ya kama hanyar almajiranci inda ya yi karatun allo da na ilimi. Yanzu haka zauren gidansu ne ya mayar makarantarsa ta allo yana koyar da yara karatun allo. (Hira da Jikansa, Murtala Usman, 18-12-2024)

Kassu Zurmi ya rasu bayan wata rashin lafiya da ya yi har ya kwanta asibitin Gwamnati na Gusau a 1987. (Gusau, 2005).

### 3.0 Hanyar Gudanar Da Bincike

Wannan bincike ya tattaro wasu waƙoƙin Kassu Zurmi ne domin gano wuraren da aka nuna cewa shi makaɗin Maza ne. An yi amfani da dabarar shiga manyan ɗakunan karatu domin bincike a kan waɗansu bayanai da manyan masana suka yi don su taimaka ma mu ƙulla zaren tunanin wannan aiki. Sannan kuma an yi hirarraki da wasu jama'a masana waƙoƙin Kassu Zurmi domin fayyace wasu matsaloli.

### 3.1 Baiwar Kassu Zurmi ta Tsara Waƙa

Tsara waƙa baiwa ce kuma sirrin mawaƙi ne da shi da zuciyarsa. An ce shahararrun mawaƙan Hausa musamman Kurna da Ɗandawa a maƙera suke zuwa hira, su zauna wurin masu zugazugai suna ɗaukar ma'aunin waƙarsu ta duban yadda ɗan zuga ke ba wuta iska. Wasu an ce su da kansu ke karɓa su yi zuga sai sun daidaita amon gindin waƙar da suke son ƙullawa su tashi. Wasu mawaƙa kuma daga kukan tsuntsaye ko motsinsu suke samun turken waƙoƙinsu. (Bunza, 2009:25).

A baiwar da Allah ya yi wa Kassu Zurmi a fagen waƙa, shi ke tsara tunaninsa da kansa, amma da ya ƙulla gindin waƙa za a ga ta raja'a ga abubuwan da muke ambato. Ba wai dole sai ya san a kan karin da ya ɗora ta ba, domin hatta da wasu shahararrun marubuta waƙoƙi ba su kula da waƙoƙinsu ya hau karin Larabci ba, balle waƙar baka. Wannan shi ne tsari na farko da anka hanga a tsarin waƙoƙin Kassu Zurmi.

Hausawa na cewa, "Shiri gamammen aiki". Duk wani aiki da mutum yake yi akwai yadda yake yi domin ya ga cewa ya tsara aiki nasa ya kuma tafi daidai yadda har zai samu karɓuwa ga jama'a. Alhaji Kassu Zurmi makaɗi ne mai cin gashin kansa, domin shi ke

kiɗansa kuma shi ke rawarsa. Ma'ana shi Kassu Zurmi ba ya da masu yi masa amshi. Har ila yau, Kassu Zurmi idan yana son ya shirya waƙa sabuwa yakan tsaya a gida yana yin wani aiki kamar noma, ko tsari na shifci (yama). Da yaransa sun ji haka sai su ce yau wata sabuwar waƙa za a yi, ko kuma idan sun ji shi yana aiki yana yin wani gurnani, to akwai zaton cewa wata sabuwar waƙa za ta ɓulla.

Haka kuma, duk a cikin tsarin waƙa da Kassu ke yi shi ne, yana iya zuwa a fagen wasa ya shirya waƙa nan take, kuma ya rera ta, ta yi daɗi da armashi. Wannan kaɗan ke nan daga cikin baiwar da Allah ya yi wa Kassu Zurmi a wajen tsara waƙa.

A bayani na gaba dangane da tsara waƙarsa kuwa yaransa sun ce idan suka ga Kassu yana wani aiki, kamar tsarin na shifci ko noma, sun ce idan zai shirya wata sabuwar waƙa ba ya magana da kowa, sai dai kawai su ji shi yana wasu gunaguni to sabuwar waƙa zai shirya. Sai dai kawai aji ya yi sabuwar waƙa.

Duk da kasancewar Kassu makaɗin matsiyata, amma yana da wata baiwar da ba matsiyata a ɗauke da shi ba. Za ka isko duk garin da ya je waƙa, yana sauka a cikin garin ko dai masarauta ɗauki baƙuncin sa ko wani attajiri ya ɗauki ɗawainiyarsa.

Wata baiwa kuma ita ce ko da yake makaɗin matsiyata a wasu lokuta shi ke ɗauke da ɗawainiyar wasu 'yan tauri domin shi mai arzikin makaɗi ne. Duk wani abu da ake iya ba makaɗin sarakuna a wancan lokacin, bai wuce a ba su dawaki ba. A zamanin da Kassu yake raye da shi ba yaransa kowa na da dokin hawa, kasancewar doki a wancan lokaci shi ne makwafin mota. (Hira da Namakka, ɗan Sakai, ɗa daga cikin ɗiyansa 20-12-2024).

### 3.1.1 Kassu Zurmi A Matsayin Makaɗin Maza

Makaɗa Kassu Zurmi a matsayinsa na makaɗin maza, ya amince da ya zaɓi ci gaba da kidan gadon gidansu na 'yantauri da 'yan farauta, watau dai kiɗan matsiyata don yana da cikakkiyar sha'awa a kan haka, musamman gani shi ma talaka ne ba wadata irin ta masu kuɗi ke gare shi ba. Kuma ya ɗaukar wa ransa, tun ba daga bisani ba, baya yi wa kowa waƙa sai su. Ashe ke nan waƙoƙin matsiyata kawai yake yi, su ne kuwa 'yan farauta da 'yan tauri da ɓarayi. Domin shi Kassu har kirari yake yi wa kansa da cewa:

Jagora: Roƙo ga wanda ba samu wahala ne,
: Sai ni kaɗai da nis saba da irinsu,
: Ni kam na saba da matcata.
(Kassu Zurmi: Waƙar Garban Ɗangido)

A nan Kassu ya nuna mana ɓaro- ɓaro cewa shi bai wa kowa waƙa sai maza kuma ko mazan sai matcata, watau daga 'yan farauta sai 'yan tauri da kuma ɓarayi.

## 4.0 Sarautar Sarkin Makaɗa

Da al'amarin kiɗa ya sami bunƙasa da shahara, saboda irin gudummuwar da Kassu Zurmi yake bayarwa a fagen kiɗa, Sarkin Zamfaran Zurmi ya naɗa shi Sarkin makaɗa maza a ƙasar Zurmi. A wannan lokaci an yi ƙasaitaccen buki wanda 'yantauri da 'yan farauta da ɓarayi da makaɗa daban- daban tare da jama'a masu ɗimbin yawa suka taru domin taya Kassu Zurmi murna. (Gusau, 2005:228).

Duk da Kassu Zurmi ya yi waƙoƙi daban- daban kamar na Noma da na farauta da na tauri da na ɓarayi, amma sanin kowane ya fi fice a wajen waƙoƙin tauri da na farauta da fawa. Duk da in an duba za a ga cewa waɗannan waƙoƙi da ya yi ba na raggo ba ne, musamman Noma da Fawa. Amma shi tauri da farauta sanin kowa ne sana'a ce ta maza. (Hira da Jikansa Mutari Usman, 18-12-2024).

Kassu a matsayinsa na makaɗin maza wanda ya iya zaɓen kalmomin da yake gina ɗiyan waƙoƙinsa da su waɗanda suke da cewa da manya da ƙananan saƙonnin da yake sakawa a cikin ɗiya ko zubin waƙoƙinsa na gaba ɗaya. Kasancewar waƙoƙin Kassu Zurmi, bisa a galab iya, na turken zuga ne da yabo. Kuma yin amfani da tsofaffin kalmomi. Misali:

Jagora: Torankawa tsiya Uban mairogo,
: Ko hwatar tai yawa takan zama iko.

Jagora: Na magaji ƙanƙari ba ka jiƙa,
: Gauɗe ba ka matanki,
: Baba kaɗe ba ka baka,
: Nomau tushen faɗa karen masu gari.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Na Magarya)

Idan anka duba a nan Kassu yana zuga da yabo ga Nomau da cewa shi matsiyaci ne bai da komi. Kuma ya yi amfani da wasu kalmomi tsofaffi a wannan ɗiya na waƙa, in da ya ambaci "hwatara" da "Gauɗe" da "Matanki".

Dangane da tsarin jimloli Kassu makaɗi na wanda yake tsara jimloli masu matsakaitan tsayi, wata sa'a kuma ya yi su dogaye, wasu lokuta ma yana shirya tarin kalmomi waɗanda ke ɗauke da aikatau a cikinsu. Misali:

Jagora: Niz zo nic ce Saraki doki nika so,
: Ku kau nac ce da tarbace za ku saye,
: Yac ce la-la-la babu ruwana,
: Kassu in don ni ko anini nau ba ya shiga,
: Nomau dai ba ya rage ma kowa Magarya,
: Sannan wani ba ya sa shi aiki shi tahi.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Na Magarya)

A nan Kassu ya yi amafni da dogayen jumloli, kuma suna ɗauke da aikatau a cikinsu. Kama kalmar "Saye". Kuma makaɗin yana amfani da karin harshen Sakkwatanci. Misali: inda ya ce "Nic ce" maimako na ce, "Niz zo" maimakon na zo.

Wani matsayi da aka nuna mana na cewa, Kassu dai lalle makaɗin maza ne shi, inda aka fito da cewa waƙoƙin 'yan tauri matciyata, su ne suka fiddo da Kassu Zurmi a fili, musamman waƙar Kassu ta Nomau na Magarya da Shayi Ɗan Gidan Labbo. Waɗannan waƙoƙi guda biyu suna daga cikin tsofaffin waƙoƙinsa na farko- farko. Ga misali daga waƙar Nomau:

Jagora: Nomau tushen hwaɗa karen masu gari,
: Torankawan tciya uban mairogo,
: Ko hwatara tai yawa to kan zama iko,
: Nomau ko ba ka jin batun masu gari?

Jagora: Na Magaji ƙanƙari ba ka jiƙa,
: Gauɗe ba ka matanki,
: Baba kaɗe ba ka baka,
: Nomau tushen hwaɗa karen masu gari.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Na Magarya)

Kassu Zurmi na yin amfani da zaɓaɓɓun kalmomin da za su nuna bajinta da ƙwazo, da kuma nuna tantagaryar tsiya da fitina da ƙuru da nuna son halakar da kai ga wanda yake zugawa. Dubi waɗannan ɗiyan waƙa ku ga yadda Kassu yake amfani da kalmomin tsiya da washi ga jaruminsa Tataccen ɗan tauri kuma gogaggen mafarauci, wato Nomau na Magarya.

Wani misali kuma da ya nuna a waƙar Shayi ɗan gidan Labbo mu ga abin da Kassu yake cewa:

Jagora: Mai kwana ya tashi,
: Mai tafiya kau ya dakata shi kau,
: Ku tashi kun ji kiɗan Shayi ɗan gidan Labbo.

Jagora: Ku hwalka na kai ga masu ɗan- gashi,
: Lalle Sha- yaya adda ɗan- gashi,
: Ya yi biɗa aure bara sai da yas samu,
: Iro ya kai ta gidan maigidansu yah hwaɗi,
: Yam mutu yab bas shi ba abin amren,
: Kana ba hatsin ɗiba.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo)

Wani matsayi da ke ga Kassu Zurmi na zama makaɗin maza, shi ne yiwa ɓarayi waƙa. misali a waƙar Mamman Ɗan Sale, Kassu na cewa:

Jagora: Karamin ɗan duniya ka tonon rairai,
: Mamman ya hwaɗa ma ƙoren mata,
: Sai ƙoƙarin ɓantala tasoshi,
: Shegen ɓarayi an nan,
: Rangama ba ta zanen suna.

Jagora: Gamshiƙa na Sani an kai ne,
: In ji kuwwa ana buzanci,
: Ih! Karenka,
: Has! Namiji,
: Muhammadu inji ka ba bugaje haushi,
: To,
: Mala'ikab bugaje,
: Ɗan Sale ciyyon cikin 'yan banza.
(Kassu Zurmi: Waƙar Mamman Ɗan Sale)

A waɗannan ɗiyan waƙa Kassu ya nuna cewa maza ne yake wasa wa inda mun ga yana koɗa gwarzon nasa, wato Mamman ɗan Sale yana yi masa kirari. Wanda kuma mun san cewa, waɗannan kalmomi da Kassu ya kawo, kamar su Rangama da Gamshiƙa duk kalmomi ne da ake koɗa maza da su.

Muhimman jigogin waƙoƙin maza sun haɗa da zuga da ta'addanci, da bajinta da kuma yabo wanda shi ne kandamin duk waɗannan jigogi. A kan haka ne za mu iya cewa, yabo cikin waƙoƙin maza ya kan ɗauki fuskoki da dama kamar yabo ta fuskar ta'addanci da yabo ta fuskar aikata wani abin kunya da yabo ta fuskar bajinta ko yabo ta fuskar fifiko wajen ƙarfi ko dibara ko asiri da makamantansu. (Yahya, 1996:86).

**Yabo Ta Fuskar Ta'addanci:** Wannan jigon an fi samun sa cikin waƙoƙin 'yan tauri, yana bayyana irin mummunar ɓarnar da wanda ake yi wa waƙa ya aikata a kuma nuna cewa a sararin duniya shi kaɗai ke iya aikata shi. Misali a cikin waƙar Nomau Na Magarya, wadda Kassu Zurmi ya yi, akwai inda yake cewa:

Jagora: Nai tambaya cikin 'yan tauri,
: Kuma nai tambaya ga manyan makaɗa,
: Wa anka wa doki da gangami ba ni ba,
: Doki da gangami sai Nomau.

Jagora: Yac ce sabad da shi za bi fashe,
: Ni ko nic ce in don sabod da ni ba ka fashe,
: Bari in ba ka shawara.

Jagora: Amsad doki gida kara mina na ga matciyaci,
: Bari sai gobe da sahe,
: Iskan nan ya taso mai kwasa sansami yana karkar,
: Sannan ɗeba wuta ga ragge ka fita.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Na Magarya)

A nan an nuna cewa Kassu yana ba gwarzon nasa cewa ya yi ta'addanci na kunna wuta ga gari. In har an ga cewa zai yi haka to za a yi tarbacen kuɗɗi a bashi, domin a sai wa Kassu doki, ya hi a ce ya yi hwashe. Kuma ya bi shawarar ta yin hakan.

## 5.0 Shaharar Kassu A Waƙa

Kafin Kassu Zurmi ya shahara wajen kiɗa da waƙa, ya fara bin mahaifinsa wajen kiɗan farauta tun yana yaro ƙarami. Bayan koyon kiɗan farauta da yake yi daga wajen mahaifinsa ya taɓa kiɗan noma, amma bai mayar da hankalinsa sosai a kansa ba. Shi dai kiɗan farauta ya gada ya taras Ubansa yana yi, don haka, ya himmatu a kansa, har Allah ya ba shi rabo mai yawa a ciki. (Gusau, 2003:225).

Kassu Zurmi ya yi kiɗan Dumma, kamin daga baya da ya goge wajen yi wa maza mafarauta da 'yan tauri da ɓarayi waƙa, sai ya juya zuwa kalangu a matsayin abin kiɗansa na maza.

Wata shahara da Kassu Zurmi yake da ita a wajen kiɗan maza ita ce, shi ba wai gidanjensu kawai yake bi idan suna ko biki ya kama ba, a'a tare da shi ake zuwa dajin farauta, duk abin da aka yi na farauta a gabansa, ba wani mai bashi labari ra'ayal aini ne shi.

Shi kansa a wasu ɗiyan waƙoƙinsa ya nuna cewa da shi ake zuwa farauta. Dubi abin da yake cewa:

Jagora: Tahiya madoka ko dajin kuna,
: Kowajji 'yan kalangaina na tahi a nan,
: Sai ɗa da ɗa ka kai naman daji.

(Kassu Zurmi: Waƙar Garu- Garu Na Magaji)

A wata shahara da Kassu ke da ita ce , shi ba ya roƙon kowa in ba matciyaci ba. Domin ya nuna cewa, shi baya sauka gidan mai samu, sai inda ba samu ne yake sauka. Mawaƙin na cewa:

Jagora: Roƙo ga wanda ba samu wahala ne,
: Sai ni kaɗai da nis saba da irinsa,
: Ni kam na saba da matcata.
(Kassu Zurmi: Waƙar Garban Ɗangido)

Duk a ciki shaharar da Kassu ya yi a fagen waƙa, akwai waƙoƙi biyu da suka ƙara fito da shi a sarari har jama'a suka san shi sosai da sosai. Waɗannan waƙoƙin su ne, waƙar Nomau Na Magarya, da kuma Waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo. Waɗannan waƙoƙi sun nuna shaharar Kassu Zurmi inda ya yi fice sosai musamman wajen yi wa maza waƙa. Kama daga 'yan farauta da 'yan tauri da kuma ɓarayi.

## 6.0 Kammalawa

Dangane da abin da aka gabatar a wannan muƙalar game da nazari a kan Kassu Zurmi a matsayin Makaɗin Maza. A cikin muƙalar an kawo hujjoji da suka kawo hakan.

A taƙaice idan muka duba lalle Kassu Zurmi ya cancanci a kira shi, makaɗin maza kamar yadda bayani ya gabata. A cikin maƙalar an kawo taƙaitaccen tarihin shi mawaƙin, an kuma duba hanyoyin da aka bi domin ganin wannan aiki ya kammala, aikin ya nuna mana baiwar da Allah ya yiwa Kassu a wajen tsara waƙarsa ta zamansa makaɗin maza. Maƙalar ta nuna cewa har sarautar makaɗin maza aka bashi. Daga ƙarshe aka kammala kuma aka kawo sunayen wasu ayyuka da aka duba, wato manazarta.

## Manazarta

Bunza, A.M. (2009) Narambaɗa. Lagos: Ibrash Islamic Publication Centre Limited.

Ɗangambo, A. (2007) Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa. Kano: Amana Publishers Limited.

Gusau, S.M. (1993) Jagoran Nazarin Waƙar Baka. Kaduna: Fisbas Media Service.

Gusau, S.M. (2002) Sarkin Taushin Salihu Jankiɗi. Kaduna: Baraka Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2005) Makaɗa da Mawaƙan Hausa. kano: Benchmark Publishers Limited

Junaidu, I, da 'Yar'aduwa, T.M. (2007) Harshe da Adabin Hausa a Kammale. Don Manyan Makarantun Sakandare. Lagos: Specturum Books Limited.

Magaji, A. (2016) Kassu Zurmi da waƙoƙinsa. Ibadan: Spectrum Books Limited.

Sarɓi, S.A. (2007) Nazarin Waƙen Hausa. Kano: Samarib Publishers.

Yahya, A.B. (2001) *Salo Asirin Waƙa*. kaduna: Fisbas Media Services.

**HIRA**

Hira da Abdullahi Birnin Magaji
Ranar Larba 18-06-2025.